# Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan ya ce: Sami'allahu liman hamidahu (Allah Yaji wanda ya gode maSa) wani ɗaya daga cikinmu baya sunkuyar da bayansa har sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya faɗi yana mai sujjada, sai muma mu faɗi muna masu sujjada a bayansa

Daga Abdullahi bn Yazid al-Khaɗmi ya ce: Bara'u ya zantar da ni alhali shi ba maƙaryaci ba ne, ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan ya ce: Sami'allahu liman hamidahu (Allah Yaji wanda ya gode maSa) wani ɗaya daga cikinmu baya sunkuyar da bayansa har sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya faɗi yana mai sujjada, sai muma mu faɗi muna masu sujjada a bayansa.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Bara'au Dan Azib - Allah Ya yarda da shi - yana bada labari alhali shi mai gaskiyane, Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance idan ya ɗago kansa daga ruku'u kuma ya ce: Sami'al lahu liman hamidahu (Allah Yaji wanda ya gode maSa), wanda ke bayansa ba ya gushewa a tsaye, kuma wani ba ya sunkuyar da bayansa dan yin sujjada har sai (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya sanya goshinsa akan ƙasa, sannan su faɗi suna masu sujjada a bayansa.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee